# Wuraren Shiryar da P/CVE

Akwai wurare masu faɗi sosai na shiryar da P/CVE, sannan za a iya ɗora wuraren shirin a bagire daban-daban (kasashe, yankuna, al'ummomi, da sauransu). Saboda haka, a yayin da ake tsara furojet na P/CVE, za a sanar da ayyukan da aka zaɓa kai tsaye daga takamammen bagiren shirin. A ƙasa, mun kawo ayyukan da za a iya yi na P/CVE a ƙarkashin azuzuwan gaba ɗaya. A cikin kowanne waɗannan azuzuwa, mun kawo misalan da ke nuna takamammun ayyukan P/CVE da ƙungiyoyi za su iya yi domin magance ƙalubalen da suke fuskanta. Ga kowanne samfurin ayyuka, mun saka bayani game da ainihin furojet ɗin da ƙungiyoyin cikin gida suka ɗabbaƙa a ko'ina cikin duniya.

Kari da misalan da muka bayyana a ƙasa, muna ba da shawarar samun ƙarin wasu bayanai 'yan kaɗan a kan shiraruwan P/CVE:

- Tushen bayanin Tasirin CVE na Tarayyar Turai
- Bayanan da aka tattara na Haɗin-guiwar Wayar da kai a kan Tsattsauran Ra'ayi
- Akwatin kaya na CVE Ofishin Shiraruwan Ba da Taimako (USAID)

## Hanyoyin Tuntuɓa na Al'umma

Hanyar tuntuɓa ta cikin gida da aka samar domin magance wasu abubuwa da lamurra na tsattsauran ra'ayin rikici a cikin al'umma, waɗanda suka bayyana suka kuma/ko kasance cikin tsattsauran ra'ayin rikici, za ta iya tasiri wajen dakile tsattsauran ra'ayin rikici, musamman idan aka ci gaba da amfani da ita na tsawon lokaci. A ƙasa, ga wasu jerin ayyukan P/CVE nan da za su iya kasancewa na al'umma.

| WURIN AIWATAR DA AIKI | BAYANI | MISALAN FUROJET |
|---|---|---|
| Ilimin Sanin Al'umma | Jin takaicin gwamnati da yawa aka dauke shi a matsayin lamarin da ke sa tsattsauran ra'ayin rikici. Akwai hanyoyi da dama na magance wannan lamari, ɗaya daga cikinsu shi ne ilimantar da mutane game da haƙƙinsu na zama ɗan'adam. Zai iya yiwuwa 'yan ƙasa ba su san haƙƙinsu ba, amma kuma wajibi ne su sani. Bugu da ƙari, sau tari ba su san yadda za su fuskanci waɗanda ke kan mulki ba game da matsalolinsu. Ta hanyar sanar da mutane ilimin sanin bil'adama, to an bai wa 'yan ƙasa ilimi da ƙwarewa na zama masu kawo sauyi a cikin al'ummominsu. | A 2016, ƙungiyar Union des Tunisiens Indépendants pour la Liberté (UTIL) ta ƙaddamar da Haɗin-guiwa ta Ilimantar da Larabawa sanin Hakkinsu. A wani ɓangare na wannan shiri, UTIL ta samar da jagora na amfani da ilimin sanin haƙƙin ɗan'adam wajen dakilewa da yakar tsattsauran ra'ayi na rikici.<br>A 2019, ƙungiyar Haɗin-guiwa na Afurka ta Yamma domin Samar da Zaman Lafiya (WANEP) reshen Mali ta ziyarci UTIL a birnin Tunis domin koyo game da Jagorar Ilimin Sanin Hakkin Ɗan'adam na UTIL. A yayin wannan ƙara wa juna ilimi na ƙwararru, UTIL da WANEP sun tattauna game da yin amfani da ilimin sanin hakkin ɗan'adam wajen dakilewa da yakar tsattsauran ra'ayi na rikici. UTIL kuma ta taimaka wa WANEP wajen saita Jagorar Ilimin Sanin Haƙƙin Ɗan'adam ya dace da mutanen ƙasar Mali.<br>Furojet na Kenya Tuna Uwezo furojet ne da USAID ke tallafa wa, wanda Al'ummar Duniya ta ɗabbaƙa, wanda kuma ya ƙunshi ilimin sanin hakkin bil'adama. Aiki da abokan hulɗa na cikin gida, irin su PeaceNet da Kituo Cha Sheria, ya sa furojet ɗin ba mazauna gari, musamman matasa, damar bayyana damuwarsu da kuma aiki wajen samun mafita bai ɗaya. |

| WURIN AIWATAR DA AIKI | BAYANI | MISALAN FUROJET |
|---|---|---|
| Yi wa Al'umma Wa'azi | Tare da ilimin sanin hakkin bil'adama, koyar da al'umma yadda za su yi wa kansu wa'azi shi ma wata hanyara ce ta yaƙi da tsattsauran ra'ayi. A lokuta da dama, mutane sukan shiga ƙungiyoyin tsattsauran ra'ayi ne saboda suna jin cewa gwamnatocinsu ba su yi musu abin da ya dace, sannan ba su san yadda za su nemi hakkinsu ba. Idan aka sanar da al'umma yadda za su nemi hakkinsu ta hanyar da ta dace kuma mai tasiri, to shiga ƙungiyoyin tsattsauran ra'ayi zai ragu. | A yankin da VE ya shafa a Diffa ta Jamhuriyyar Nijar, USAID/OTI sun tallafa wa ci gaban haɗin-guiwa na shugabannin al'ummomi na 12 domin ƙange shiga ƙungiyoyin tsattsauran ra'ayi a yankin, waɗanda Boko Haram da ISIS ta Yammacin Afurka suka shafa. Haɗin-guiwa na [Nalewa Mada]() ("Zaman lafiya Muke Nema"), a yanzu ya ƙunshi ƙauyuka 30 tare da matasa fiye da 300, da mata, da kuma shugabannin gargajiya da na addini.<br><br>A 2017, [Kungiyar 'Yan'uwa ta IDMAJ]() ta gudanar da taron ƙara wa juna sani na kwana uku a Kasabalanka, ƙasar Maroko ga mutane 40 da suka fito daga ƙungiyoyin farar hula, ƙungiyoyin al'umma, da makarantun addini da na ilimi daga wurare daban-daban na Kasabalanka. Manufofin taron na ƙara wa juna sani su ne: (1) sanar da shugabanni daga waɗannan makarantu game da ƙungiyoyi da haɗin-guiwa na tsattsauran ra'ayin rikici; (2) tattauna ma'aunan daƙile tsattsauran ra'ayi; da (3) samar da dandali domin babban haɗin guiwa domin yaƙi da shigar su. Bayan watanni huɗu, IDMAJ ta sake aiwatar da taron ƙara wa juna sani na biyu ga wakilan CSO domin gano hanyoyin da ake shiga ƙungiyoyin da kuma hanyoyin magance tsattsauran ra'ayin rikici a mazaunar Sidi Moumen da ke Kasabalanka. Tare da jagoranci daga IDMAJ, mahalarta taron sun ƙirƙiri rukunai biyar a matakin wayar da kan al'umma, waɗanda kuma suka ci gaba da aiki a koyaushe a Sidi Moumen, domin ilimantarwa da wayar da kai game da tsattsauran ra'ayin rikici. |
| Tsarin Cikin Gida na Damawa da Al'umma | Hanyoyin jagorancin al'umma da tsarin cikin gida sun tabbatar da cewa hanyoyi ne masu tasiri na damawa da masu ruwa da tsaki da dama daga al'ummomin cikin gida. Damawa da masu ruwa da tsaki masu yawa daban-daban sau tari yake da muhimmanci wajen fahimta da kuma daƙile tsattsauran ra'ayin rikici. Ta ɗabbaka ayyukan da al'umma za ta jagoranta, to an karfafa masu ruwa da tsaki na cikin gida, an inganta damarsu ta magance tsattsauran ra'ayin rikici, sannan an kara ɗinke al'umma daga shiga tsattsauran ra'ayin rikici. | A 2019, [Kungiyar Malienne Pour La Survie Au Sahel]() (AMSS) sun yi taron ƙara wa juna sani game da ƙarfafa kauce wa tsattsauran ra'ayi da dangantakar cikin gida na al'ummomi biyu (Rharous da Séréré) a yankin Timbuktu na ƙasar Mali. Mahalarta taron sun haɗa da matasa, mata, jami'an da aka zaɓa, 'yan jarida, sarakunan gargajiya, shugabannin addini, magabata da wakilan CSO. Lokacin kowane taro, AMSS sun yi amfani da hanyar damawa da masu ruwa da tsaki da yawa ([SCALE+]()) domin gano matakai da ayyukan da suka dace domin habaka daƙile VE a waɗannan al'ummomi. Saboda haka AMSS sun taimaka wa mambobin al'umma wajen ɗabbaka ayyuka uku na kaucewar al'umma daga bin tafarkin tsattsauran ra'ayi, da suka haɗa da: (1) tawagar da ta wayar da kai cikin matasa game tsattsauran ra'ayin rikici ta hanyar shirya wasannin motsa jiki; (2) bayani da wayar da kai game da taro na ƙara wa juna sani a kan rawar da mata ke takawa wajen daƙile faɗa da tsattsauran ra'ayin rikici a cikin al'ummarsu; da kuma (3) taron ƙara wa juna ilimi na gina iya aiki domin wayar da kai game da halartar shiraruwan P/CVE.<br><br>Sauran bayanai da/ko furojet-furojet game da tsarin damawa da al'umma:<br>• [Rawar da Kungiyoyin Farar Hula ke takawa wajen Dakilewa da Yaki da Tsattsauran Ra'ayin Rikici da Tsattsauran Ra'ayin da ke Kai wa ga Ta'addanci]() (OSCE)<br>• [Wurare masu kariya:Sabuntaccen Akwatin kaya domin Karfafa Al'umma da Magance Tunanin Tayar da Rikici]() (Hukumar Lamurran Al'umma na Musulunci)<br>• [Ma3an](), Tunisia (FHI 360)<br>• [Sanad na Wanzar da Zaman Lafiya](), Iraki (USIP) |

| WURIN AIWATAR DA AIKI | BAYANI | MISALAN FUROJET |
|---|---|---|
| Aikin 'yan sanda Al'umma | Bayyanannen tsaro lamari ne a cikin al'umma inda ɗaiɗaikun mutane ke saukin kamuwa da tsattsauran ra'ayin rikici. A waɗannan misalai, samar da shirin aikin 'yan sandar al'umma hanya ce mai tasiri wajen magance rashin tsaro. Shiraruwan aikin 'yan sandan al'umma sukan mayar da hankali ne wajen gina dangantaka mai kyau tsakanin 'yan sanda da al'ummar gida da aka gina a kan gaskiya da girmamawa. | Kimanta halartar matasa a shirin USAID da aka gudanar a 2015 a Tangier da Tetouan (ƙasar Maroko) ya nuna cewa, rashin tsaro tsakanin matasa a mazaunansu za a iya danganta shi da rashin wanzuwar tsaro a wuraren. Domin ƙarfafa halartar kowa da kowa, Gwamnatin Maroko ta shiga shirya sauye-sauye da suka ba da fifiko ga damawa da 'yan sanda kaitsaye, da hukumomin cikin gida, da 'yan ƙasa domin su sami biyan bukatocinsu yadda ya fi dacewa da kuma inganta tasirin jami'an tsaro na gaba ɗaya. USAID kan tallafa wa ƙoƙarin gwamnati na kawo sauyi ta hanyar Aikin 'Yansanda na Wayar da kan Al'umma (COPA) furojet na wucen-gadi. Gabanin fara furojet, waɗanda ke zama a mazaunan da ake son cim ma wa ba su tattauna damuwarsu na kariya da tsaro ba a bayyane. Ta hanyar COPA, waɗannan ɗaiɗaikun mutane suka manta da bambance-bambancen da ke tsakaninsu domin koyon sababbin abubuwa da ba da gudummuwarsu wajen inganta tsaro a cikin al'ummominsu. USAID na samar da ƙwarewar 'yansanda da mazauna gari domin taimaka musu ga yin aiki tare wajen magance matsalolin kariya.<br><br>Wasu muhimman bayanai da/ko shiraruwa game da aikin 'yansandan al'umma:<br><br>• Dakile Ta'addanci da Yaki da Tsattsauran Ra'ayin Rikici da Tsattsauran Ra'ayin da ke Kai wa ga Ta'addanci:Hanyar Aikin 'Yansandan Al'umma (OSCE)<br>• Aikin 'Yansandan Al'umma a Bangaladash (Asusun Nahiyar Asiya)<br>• Aikin 'Yansandan Al'umma a Bangaladash (Asusun Nahiyar Asiya) |
| Dabarun Al'umma wajen Dakile Tsattsauran Ra'ayin Rikici | Yayin ɗaukar hanyar tsarin cikin ga P/CVE, mataki na farko shi ne tattara mambobin al'umma da samar da dabarun al'umma. Ta hanyar saka muryoyin cikin gida, ƙalubale da hanyoyin magance su za su kasance masu alaƙa da al'umma. Ta farawa da hanyar da al'umma ke jagoranci, akwai yiwuwar ƙaruwar shigar 'yan cikin gida cikin shirin P/CVE, wanda zai iya kai wa ga muhimmin tasiri na shirin. | Ayyukan Kenya NiWajibu Wetu (NIWETU), da USAID suka tallafa wa sannan DAI suka ɗabbaƙa, sukan ƙarfafa Kungiyoyin Farar Hula da masu-faɗa-a-ji a cikin al'umma wajen jagorancin shiraruwan CVE.  Tun 2016, NIWETU ta ƙulla hulɗa da ƙungiyoyi 39 na cikin gida domin su haɗa hannu wajen tsara takamammun ayyukan da suka shafi bagire a duk faɗin Kenya.  NIWETU takan kuma tallafa wa Zakarun Kawo Sauyi (C4Cs) guda 52 a faɗin gundumomi biyar a ƙasar Kenya ta hanyar horaswa, jagoranci, da kuma ci gaba da bayar da taimako na ƙwarewa.<br><br>A 2016, Kungiyar Chifae ta ɗabbaƙa horaswa ta kwana biyu ga masu bincike 52, 'yan rajin ƙungiyoyin farar hula, hukumomin jama'a, 'yansanda, da 'yan kasuwa domin samar da dabara ta dakilewa da rage tsattsauran ra'ayi wanda ke kai wa ga tsattsauran ra'ayin rikici a Tangier, ƙasar Maroko. Bayar da giɓi wajen fahimtar lamurran da ke kawo tsattsauran ra'ayin rikici a tsakanin masu ruwa da tsaki a Tangier, da kuma rashin samar da gamsassun hanyoyin magance matsalar, horaswar tana ƙarfafa ƙoƙarin masu aikin cikin gida wajen ƙara tasirin furojet-furojet na dakile VE ɗinsu.<br><br>Wasu muhimman bayanai da/ko shiraruwa game da aikin 'yansandan al'umma:<br><br>• Samar da Ci Gaban Hanyar Jagorancin Al'umma wajen Yaki da Tsattsauran Ra'ayin Rikici (Kungiyar Duniya ta Ci Gaban Bayanai da Ilimi |

| WURIN AIWATAR DA AIKI | BAYANI | MISALAN FUROJET |
|---|---|---|
| Karfafa Koƙarin Shugabannin cikin gida game da CVE | Ci gaban hanyar saka al'umma zai iya haɗawa da ƙulla hulɗeɗeniya tare da gina koƙarin shugabannin cikin gida, kamar jami'an cikin birni, malamai, dattawan ƙauye ko mutanen da suka kafu a cikin al'umma. Waɗannan shugabannin sun mallaki matakan mulki daban-daban da tasiri, ko da kuwa mulki ne na zabe a hukumance ko na mulkin da mutum ya samu sakamakon girmamawa. Waɗannan shugabannin za su iya kasancewa masu ƙarfin mulki a cikin al'umma sannan za su ƙara tasirin ayyukan P/CVE. | A 2016, Ma'aikatar Harkokin Waje ta Amurka ta bayar da tallafin ICMA domin ɗabbaƙa Gina Kwarewar CVE domin Hukumomin Birni a Yammacin Kasashen Balkans, furojet ɗin da aka tsara domin ƙulla hulɗeɗeniya tsakanin gwamnati, ƙungiyoyin farar hula, da ɓangarori masu zaman kansu domin ƙara damawa da al'umma da daƙile tsattsauran ra'ayin rikici. Furojet ɗin ya nemi yin haɗin-guiwa, horaswa, da wayar da kan magazayyan garuruwa da shugabannin birni a duk faɗin yankin Yammacin ƙasashen Balkans domin ganowa da magance haɗurran da ke da alaƙa da tsattsauran ra'ayin rikici ta hanyar shiga cikin Haɗin-guiwa na Birane Masu Karfi. Tawagar furojet ta gudanar da zagayen tuntuɓa wadda ta ƙunshi tarurruka 85 da damawa da ƙananan hukumomi guda 58. Sun shirya tarurrukan ƙara wa juna sani kan gina ƙoƙari ga mahalarta 236 a ƙasashe huɗu daga cikin shida da kuma taron yanki na ƙarshe ga biranen dukkan ƙasashe shida, da ya sami halartar mahalarta 107 daga ƙananan hukumomi 28. Bayanan kafin taro da bayansa sun nuna ƙaruwar ilimi a kan CVE da kuma yakinin ba da gudummuwa ga ƙoƙarin kasa da ƙasashen duniya wajen yaki da tsattsauran ra'ayin rikici. |

## Kafafen Yaɗa Labarai da Sadarwa

Wata hanya ta baiɗaya domin magance tsattsauran ra'ayin rikici ita ce ta kafafen yaɗa labarai da sadarwa. Akwai tashoshi daban-daban na kafafen yaɗa labarai da na'urorin fasaha da ake iya amfani da su ga ayyukan sadarwa, kowannensu za a iya sake saita shi zuwa ga siffofin VE na cikin gida. Burin waɗannan ayyuka sun fara ne da amon muryoyin shugabannin tsaka-tsaki, samar da saƙonni zuwa ga waɗanda ake ƙoƙarin sakawa cikin VEO, ƙaryatawa kai tsaye labaran VEO, da/ko gudanar da shiraruwa na al'adu daban-daban. A ƙasa, ga wasu misalai nan na ayyukan sadarwa da ake iya amfani da su ga P/CVE.

| WURIN AIWATAR DA AIKI | BAYANI | MISALAN FUROJET |
|---|---|---|
| Amon Muryoyin Tsaka-tsaki | Shiraruwan sadarwa da dama na da manufar gina ɗinkakkiyar al'umma ta cikin gida domin rashin tasirin tsattsauran ra'ayi. Hanya ta farko ta yin haka ita ce ta amon muryoyin tsaka-tsaki a wuraren da ke fuskantar tsattsauran ra'ayin rikici. | Furojet ɗinMuryoyin Somali a Kenya, da ƙungiyar Equal Access ta ɗabbaƙa, ya mayar da hankali ne a kan yawan jama'ar Somali a gundumomin Nairobi da Wajir da Garissa a arewa maso gabas na Kenya. Furojet ɗin yakan tallafa wa masu ƙoƙari wajen yin tasiri a cikin gida, da suka haɗa da matasa, dattijai, shugabannin addini, da shugabannin mata domin gina al'umma mai daƙile saƙonnin masu tsattsauran ra'ayi da tsara saƙonni masu fa'ida da kuma kamfen na wayar da kan al'umma.<br>Sauran misalai:<br>• Muryoyin Zaman Lafiyaa Afurka ta Yamma |

| WURIN AIWATAR DA AIKI | BAYANI | MISALAN FUROJET |
|---|---|---|
| Madadin Labarai | Ingantattun labarai sukan zama madadin ƙunshiyar tsattsauran ra'ayi, ba kamar yaki da saƙonnin tsattsauran ra'ayin rikici kaitsaye ba.  Ana iya amfani da na'urorin sadarwa da dama wajen yaɗa madadin labarai da dama, sannan ita ce hanyar da ta fi dacewa wajen amfani da na'urori (misali, TV, radiyo, Facebook, SMS), da suka haɗa da waɗancan na'urori da VEO suka yi amfani da su, domin cim ma waɗanda ake son cim ma. | Salam Shababwasan kwaikwayo ne na TV domin matasa a Iraƙi da ya sami lambar yabo wajen gina zaman lafiya. Bisa ga manhajar ilimi, wasan kwaikwayon na talabiji ya haɗa kan matasan Iraƙi da su yi gasa a ƙalubale hudu (gajeren fim, wasanni, na hankali, dirama). Tawagar da ta yi nasara ta sami wakilcin matasa daga wurare daban-daban na ƙasar, da ƙarfafa musu guiwa da yin aiki tare domin samun nasara. Ta yin haka, sun nuna waɗannan ɗabi'u ga matasan da ke kallon talabijin. Jerin wasannin kwaikwayon da aka nuna a tashoshin talabijin da dama a Iraƙi daga 2009-2013, sun  da matasa a dukkanin Gabas ta Tsakiya a kan kafafen sa da zumunta sannan sun gina kaucewar matasa daga bin tafarkin tsattsauran ra'ayin rikici.<br>Sauran misalai:<br>• Dandalin Madadin Saƙonni na Ourmindanow a kasar Philippines<br>• Farar Tattabaraa Arewacin Nijeriya da Bakin Tafkin Chadi<br>• Hirka Nabadda a Somaliya<br>• Kauye Ɗaya, Muryoyi Dubu a Afghanistan |
| Yaki da Labaran Tsattsauran Ra'ayin Rikici | "Yaƙar" saƙonnin VE za a iya kallon sa a matsayin kama dokar da ta shafi kowace nau'in sadarwa da ke yaɗa ƙunshiyar saƙonnin masu tsattsauran ra'ayi, da suka haɗa da saƙonnin madadi.  Saboda haka, yaƙar saƙonnin dole ne ya kasance yana ba da amsa ga dukkan labaran da ke haɓaka tsattsauran ra'ayi tare da ƙaryata su. | Furojet ɗin BRAVE a Kenya yakan wayar da kan shugabannin addini da sauran mambobin al'umma wajen samar da tsarin da ke yaƙar labarai da saƙonnin masu tsattsauran ra'ayin rikici. Aiki da shugabannin Musulunci, Kiristanci da masu addinai daban, furojet ɗin ya samar da horaswa da kayan aiki ga ƙungiyoyin addini a kan yadda za su yaki tsattsauran ra'ayi na labaran kan intanet ta hanyar fassara littattafai masu tsarki ta yadda ya dace.<br>Sauran misalai:<br>• #NotAnotherBrother a Siriya<br>• Burka Avenger a Pakistan<br>• Tirela ta fim ɗin Iman a Sudan |
| Sadarwar Sauyin Al'umma da Ɗabi'unsu (SBCC) | SBCC wata hanya ce ta amfani da hanyoyin sadarwa wajen bunƙasa sauye-sauye a harkar ilimi, ɗabi'u, al'adu, imani da halaye. Wannan zai iya kasancewa ga dukkan jigogi, da suka haɗa da lafiya, ilimi da P/CVE. | A Maroko, Kungiyar Chifae ta fahimci cewa ilimantar da iyaye, sanar da su da kuma wayar musu da kai da ma waɗanda suka kasance a ilimantar da mutane ba za su isa ba wajen wayar da kan al'umma da matasa a wajen yaki da VE. Kungiyar Chifae ta horas da ma'aikan al'umma da na ilimi game da dabaru na sadarwa da al'umma, sannan ta ɗabbaka kamfe na wayar da kai game da tsattsauran ra'ayin rikici a tsakanin jama'a cikin Beni Makkada.<br>Sauran misalai:<br>• Tawaga (Kenya, Tanzaniya, Indonishiya) |

| WURIN AIWATAR DA AIKI | BAYANI | MISALAN FUROJET |
|---|---|---|
| Shiraruwan Tsakanin Al'adu | Shirya shiraruwan da suka shafi mabambantan al'adu wata hanya ce mai tasiri wajen gina haƙuri da gaskiya tsakanin mutane, wanda ke ƙarfafa haɗin kan jama'a da kaucewar al'umma daga VE. Shiraruwa za su iya aiki a matsayin wuraren da mutane za su gano hanyoyin haɗa kai a cikin al'ummominsu. Ire-iren waɗannan shiraruwa suna da muhimmanci musamman a cikin al'ummomin da masu tsattsauran ra'ayin rikici suka haddasa rarrabuwarsu. | Ta hanyar Zaman Lafiya ta hanyar Furojet Na Ci Gaba, Kungiyar pour la Dialogue entre les Jeunes des Diverses Religions (ADJR) a ƙasar Chadi ta gudanar da shiraruwa a tsakanin addinai domin haɗin kan matasan da ke da bambance-bambance. Mahalarta sun koyi darussa na sanin yadda za su shirya shiraruwa a tsakanin addinai a cikin al'ummominsu. A karshen kowane shiri, ADJR ta yi balaguro zuwa kowane yanki domin yaɗa darussan da aka koya tare da al'ummomi.  Mahalarta daga kowane yanki sun samar da tsari na watsa saƙonni zuwa ga al'ummominsu, da suka haɗa da shiraruwan rediyo, shirya mahawara a makarantu, da kuma dirama. Alal misali, matasan da suka halarta sun ziyarci makarantu domin tattauna yin haƙuri, zaman lafiya, da kuma faɗa a tsakanin ɗalibai a makarantu.<br>Sauran misalai:<br>• Furojet ɗin Gina Zaman Lafiya a Yemen |

## Karin Bayanai game da Kafafen Yaɗa Labarai da Sadarwa domin P/CVE:

- Laburaren Yaƙar Labarai (Cibiyar Hedayah)
- Littafin Yaƙar Labarai (Makarantar Dabarun Shiraruwa)

## Ilimi

A Disambar 2015, Sakatare-Janar na Majalisar Ɗinkin Duniya ya saki Tsarin Matakan Daƙile Tsattsauran Ra'ayin Rikici, wanda ya yi kira da kammalalliyar hanya magance yanayin da ke sa mutane tsattsauran ra'ayin rikici. A tsarin, Majalisar Ɗinkin Duniya ta ba da karfi sosai a kan ilimi, saboda za a iya amfani da ilimi ta hanyoyi da dama domin yaki da tsattsauran ra'ayi.  Ga wasu 'yan misalai nan a kasa.

| WURIN AIWATAR DA AIKI | BAYANI | MISALAN FUROJET |
|---|---|---|
| Tunani Maikyau da Gina Kwarewa | Rashin tunani maikyau da rashin ƙwarewar da ta dace zai iya kai matasa da samun tsattsauran ra'ayi. Shiraruwan da suka mayar da hankali a kan gina kauce wa tsattsauran ra'ayi ta hanyar ilimin da ke sa tunani maikyau da ƙwarewa za su iya taimaka wa wajen magance wannan matsala. | Kusan rabin al'ummar Mali 'yan ƙasa da shekara 18 da matasan da ba su aiki fiye da kashi 15, matasan Mali suna da 'yar ƙaramar dama ne ta samun aikin da ya dace. Manyan matakan rashin ilimi da rashin aikin yi ya kai ga yin kaura da rashin tausayi. EDC sun taimaki matasan ƙauyuka a Mali wajen samun ƙwarewa ta hanyar PAJE-Nièta (Projet d'Appui aux Jeunes Entrepreneurs), ko Furojet na Matasan da Ba Su zuwa Makaranta. EDC sun yi aiki da matasan da ke ƙauyuka wajen taimaka musu su zama masu ilimi, masu tsayuwa da kansu, sannan masu shiga harkokin farar hula. |

| WURIN AIWATAR DA AIKI | BAYANI | MISALAN FUROJET |
|---|---|---|
| Ilimin Zaman Lafiya | Kari da ƙunshiyar haɗaka ta P/CVE a cikin manhajar ilimi ta ƙasa, shiraruwan da suka mayar da hankalin a kan ilimin zaman lafiya za su iya taimaka wa wajen kawar da tsattsauran ra'ayi. A al'ummomin da ake da rikici na faɗace-faɗace, ilimin zaman lafiya zai iya ƙwantar da tarzoma. Shiraruwan ilimin zaman lafiya sukan mayar da hankali ne a kan ƙwarewar rayuwa kamar tattaunawa, magance matsala, dakuma saurare koyaushe, saboda haka mahalarta za su iya shiga darussa koyon lamurran rayuwarsu ta yau da kullum, ciki har da maganace tsattsauran ra'ayin rikici. | Tun 2014, USIP ta yi aiki kusa-da-kusa da makarantu a Afghanistan domin bunƙasa Ilimin Zaman Lafiya. USIP ta fara aiki da jami'o'in gwamnati da na kuɗi da kuma Ma'aikatar Ilimin Koli ta Afghanistan (MoHE) domin samar da manhajar nazarin zaman lafiya da rikici da za a iya koyarwa a jami'o'in ƙasar. Bugu da ƙari, USIP ta jagoranci ɗalibai da tsangaya a jami'o'in da suke da hulɗa wajen samar ƙungiyoyin zaman lafiya, wandaya sanya ɗalibai shiga ayyuka da lamurran bunkasa haɗin kai da zaman lafiya a tsakanin al'ummomin da ke jami'o'i daban-daban. A 2015, USIP ta ƙulla hulɗa da Kungiyar Taimakon Yaran Afghanistan (HTAC), tare da haɗakar Ma'aikatar Ilimi ta Afghanistan, domin samar da manhajar ilimin zaman lafiya ga 'yan aji 7-12. Daga wannan lokaci HTAC ta horas da malamai 1,800 daga kwalej-kwalej shida na horas da malamai da ke Parwan, birnin Kabul da yankunan Nangarhar domin koyar da ilimin zaman lafiya. |
| Kulla hulɗa da Makarantun Ilimin Addinai | A al'ummomi da dama, ilimin addinai babban bangare ne na manhajar ilimi. A wasu lokuta, umarnin addinai shi ne babba ko shi kaɗai ne tushe na ilimi. A al'ummomi irin waɗannan, ƙulla hulɗa da makarantun da suke na addini zai iya taimaka wa wajen magance tsattsauran ra'ayi. Bugu da ƙari, ta hanyar waɗannan ƙulla hulɗa ne, shiraruwa za su iya fitowa da hasashe na baiɗaya kan cewa, tsattsauran ra'ayin rikici yana da alaƙa da addini, da kuma musanta haka da cewa, makarantun addini suna tasiri ne kawai wajen daƙile tsattsauran ra'ayin rikici. | Mafi yawan matasan da ba su da tausayi a Chadi sun halarci makarantun Kur'ani ne, ba su yi makarantun bangare da ya shafi ilimin boko ba. Tare da taimakon Ofishin Jakadancin Amurka a birnin Injamena, Makarantar Salam ta ɗabbaka furojet ɗin Sanya Kyawawan Ɗabi'un Mutane Da Ilimin Ma'amala a Makarantun Kur'ani na Chadi wanda ya mayar da hankali wajen haɓaka cibiyoyin rayuwar al'umma da kauce wa bin tafarkin tsattsauran ra'ayi. Furojet ɗin ya dama da shugabannin cikin gida masu ra'ayi kamar malamin makarantar Kur'ani wanda yake da babban tasiri ga matasan da aka mamaye daga cikin al'ummomi, mafi sauƙin kamuwa ga mutane, tattalin arziki, da siyasar lamurran da ke kawo tsattsauran ra'ayin rikici. Makarantar Salam ta samar da horaswa da taimakon da ya biyo baya ga fiye da malaman makarantar Kur'ani 200 a unguwanni fiye da goma.<br><br>Sauran bayanai da/ko shiraruwa game da ƙulla hulɗa da makarantun ilimin addinai:<br>• Bunƙasa Zaman Lafiya a Makarantun Islamiya (Saƙon Kasa da ƙasa)<br>• MAKI a Kenya |

## Karin Bayanai game da Ilimi da P/CVE:

- Ayyukan da suka Fito Fili gun Tsarawa, Dubawa da Kimantawa ga Ilimin Shiraruwan Zaman Lafiya (Search for Common Ground)
- Taron Kara wa juna sani na Kasa na Gina Kokari game da Daƙile Tsattsauran ra'ayin rikici ta hanyar Ilimi a Uganda (Hedayah)
- Jagoran Jagorancin Matasa a kan Daƙile Tsattsauran Ra'ayin Rikici ta hanyar Ilimi (UNESCO)
- Daƙile Tsattsauran Ra'ayin Rikici ta hanyar Ilimi:Jagora ga Masu Shata Dokoki (UNESCO)
- Jagora ga Malami a kan Daƙile Tsattsauran Ra'ayin Rikici (UNESCO)
- Daƙile Tsattsauran Ra'ayin Rikici:Gabatarwa game da Ilimi da Daƙile Tsattsauran Ra'ayin Rikici(Haɗin-guiwa na hukumomi daban-daban game da Ilimi a Yanayin Gaggawa

## Damawa da Masu Tasiri

Yayin aiki domin daƙilewa ko yaƙi da tsattsauran ra'ayin rikici, da ya ƙunshi ɗaiɗaikun mutane waɗanda suke da tasiri zai iya kasancewa hanya mai tasiri. Masu tasiri suna iya kasancewa iyalai, mambobin al'umma, tsara, ko ɗaiɗaikun mutane da suka yi suna. Masu tasiri za su iya taimaka wa wajen sauya ɗabi'u ko ɗaukar matakin waɗannan da ke son faɗa wa hanyar tsattsauran ra'ayin rikici. Akwai hanyoyi da dama da ake iya damawa da masu tasiri. Ga wasu 'yan misalai nan a kasa.

| WURIN AIWATAR DA AIKI | BAYANI | MISALAN FUROJET |
|---|---|---|
| Damawa da Iyali | Iyali na matuƙatar taimaka wa idan aka dama da su wajen maganace tsattsauran ra'ayin rikici. Damawar da su zai iya haɗa wa da ilimantar da iyaye game da abubuwa da ke kawo tsattsauran ra'ayin rikici a tsakanin matasa da kuma ilimantar da iyaye su fahimci alamun tsattsauran ra'ayi da yadda za su dinga sadarwa da 'ya'yansu. Wani zabin kuma shi ne tsara bayanan al'umma domin iyali, kamar layin kira ko ƙungiyoyin taimako inda za su iya bayyana damuwarsu idan sun san wani yana shirin sauya halinsa. | Kungiyar Mata Zalla ta Kasa da Kasa (WwB) sun gabatar da tsari na Iyaye Daƙile Tsattsauran Ra'ayi daga Iyaye Mata (MPVE) ta hanyar furojet-furojet ɗinta na haɗin-guiwar SAVE a 2008. WwB sun samar sun kuma tsara Makarantun Iyaye Mata na farko: Tarbiyyar Yara domin Zaman Lafiya Wannan hanyar daƙilewa ta damu ne da iyaye su kasance madogara ta farko wajen kiyaye haɗurra a cikin al'umma. Manhajar ta ƙarfafa ƙoƙarin ɗaiɗaikun mata, abin da suke iya yi, da iliminsu na shauki, da zaburad da wayar da kansu game da tasirin tsattsauran ra'ayi. WwB ta ɗauki wannan shiri sannan ta dama da dubban iyaye mata daga ƙasashe goma shabiyu na Yammaci da Gabascin Turai; Tsakiya da Kudanci, da Kudu maso Gabas na Asiya; Gabas ta Tsakiya; da Yankin Afurka na Kudu da Sahara. Makarantun Iyaye Mata sun ɗaga darajar ayyukan da ke akwai na al'umma da ƙoƙarin cikin gida ta hanyar samar da masu ruwa da tsaki na ƙungiyoyin farar hula a yankun da ke cikin haɗari tare da tsari mai kyau, kayan aiki, da ƙwarewa ta yaƙi da tunanin tsattsauran ra'ayi.<br><br>Sauran misalai:<br>• Iyalai Masu Yaki da Ta'addanci da Tsattsauran Ra'ayi (duniya) |
| Damawa da Mutanen Addinai | Ɗaiɗaikun mutane na iya kasancewa cikin ƙungiyoyin masu tsattsauran ra'ayi saboda dubunnan dalilai. Wani dalili na baiɗaya shi ne neman yarda ta addini, ilimi ko buƙatar samun wani babban rabo. Shugabannin addini aka girmama su sosai a cikin al'umma sannan suna da tasiri sosai a kan mabiyansu. A sakamakon haka, shugabannin addinai abokan hulɗa ne masu tasiri sosai a shiraruwa ko dai ta daƙilewa ko sauyin tsattsauran ra'ayin rikici. | Furojet na Sadaqa ya yi aiki da Ma'aikatar Lamurran Addinin Musulunci (MoIA) domin bunƙasa zaman lafiya da haƙuri a ƙasar Mauritaniya ta hanyar ƙarfafa manyan abubuwan da ake buƙata wajen yaki da tsattsauran ra'ayin rikici. Wannan ɗan takaitaccen aiki ya ƙulla hulɗa da MoIA domin samar da dabaru da hanyoyi na taimaka wa al'umma waɗanda matasansu ke fuskantar babban haɗarin shiga ayyukan VEO. Furojet ɗin ya samar wa MoIA ƙwarewa ta shirya tarurrukan jama'a, sulhunta rikici, damawa da matasa, gano haɗurran tsattsauran ra'ayin rikici, da kafafen yaɗa labarai da sadarwa. Furojet ɗin ya taimaka wa MoIA wajen yin amfani da wannan ƙwarewa a yaki da tsattsauran ra'ayin rikici tare da masu ruwa da tsaki daban-daban. A sakamakon haka, MoIA ta faɗaɗa yankuna tare da inganta ƙoƙarinta na aiki da shugabannin addini na cikin gida da shugabannin al'umma yadda ya dace domin bunƙasa zaman lafiya da haƙuri.<br><br>Sauran bayanai da/ko shiraruwa game da ƙulla hulɗa da masu addinai:<br>• Shigar da Addini da Masu Addini wajen Yaki da Tsattsauran Ra'ayin Rikici (USIP)<br>• Cibiyar Sulhunta Addinai Daban-daban (Nijeriya) |

## Ayyukan P/CVE da suka Shafi Jinsi

Duk da cewa, furojet-furojet na P/CVE sun fi ba da ƙarfi ne ga rawar da maza ke takawa, mata ma za su iya kasancewa masu taka rawa a wajen tsattsauran ra'ayin rikici. Za su iya kasancewa masu shigar da mutane, masu tausayawa, da masu sauya hali, amma kuma za su iya kasancewa masu tasiri sosai wajen gina zaman lafiya da kuma shugabanni masu dakile rikici. Ayyukan P/CVE dole ne su bambance tsakanin bukatu da abubuwan da 'yan mata da matasa suka ba fifiko domin samar musu da damammaki da za su amfani kokarinsu da gudummuwarsu.  Domin hana mata shiga tsattsauran ra'ayin rikici, za a iya samar da ayyukan da suka kebanci jinsi da dama. Ga wasu misalai nan a kasa:

| WURIN AIWATAR DA AIKI | BAYANI | MISALAN FUROJET |
|---|---|---|
| Shigar da Mata da 'Yanmata a matsayin Masu Tasiri | Mata suna matuƙar taka rawa a ƙokarin dakile P/CVE a cikin gida saboda suna da ilimi sannan suna maganganu masu muhimmanci a cikin al'ummominsu da cikin iyalansu. Saboda haka, mata su ne suka fi dacewa wajen gano alamomi na tsattsauran ra'ayi da kuma hana VE a cikin iyalansu da al'ummominsu. Za su kuma iya taka rawa wajen wayar da kan mata 'yan uwansu na gida, da gina ƙokarinsu – wato aiki tukuru-tasiri ninkin-ba-ninkin a cikin al'ummomin da tsattsauran ra'ayi da shigar sa za su iya aukuwa. | Furojet ɗin Yaki da Tsattsauran Ra'ayi a Kawar Maila ya ƙuduri ƙirkirar hanyoyin magance ko yaki da tsattsauran ra'ayi a arewa maso gabas na Nijeriya, yankin da ya sha wahalar shigar da mutane cikin ƙungiyar Boko Haram. Furojet ɗin yakan yi aiki domin taimaka wa shugabancin mata wajen habaka hakki, zaman lafiya da tsaron ɗan'adam da fata na ƙara shugabncin mata, samar da dandali na koyo tsakanin ƙungiyoyin farar hula na cikin gida, NGOs da abokan hulɗar gwamnati, haka kuma da a tsakanin 'yan rajin kare hakki a Nijeriya da makwabtan ƙasashe.<br>Sauran misalai:<br>• Mata Masu Iko, Al'ummomi Masu Zaman Lafiya (Matan Majalisar Ɗinkin Duniya)<br>• STRIVE (Royal United Services Institute) |
| Bunkasa Hakkin Ɗan'adam da Daidaiton Mata da 'Yanmata | Bunkasawa da kare haƙkin mata da 'yan mata wani bangare ne mai muhimmanci na dakile tsattsauran ra'ayin rikici. Tauye haƙkin mata da ƙananan yara lamari ne da ya yi fice a cikin al'umma tare da shigar da su cikin ƙungiyoyin tsattsauran ra'ayi na rikici.  Ta hanyar yin aiki domin ƙwato musu haƙkinsu, mata za su iya samun saukin kasance da tsattsauran ra'ayin rikici. Ta hanyar ƙarfafa wa mata a cikin al'umma, yakan kasa musu kokari wajen dakile ayyukan P/CVE sannan su kasance masu tasiri a cikin al'ummominsu. | A 2016, ƙungiyar Search for Common Ground ta yi aiki tare da Rabita Mohammadia ta Ulemas domin ɗabbaka furojet na Ayarin Mata domin Zaman Lafiya, wanda ya kawo shiraruwan da suka sami jagorancin ƙungiyoyin farar hula da mutanen da ba su da yawa a arewacin Maroko, da suka haɗa da biranen Nador, Al Hoceima, Tétouan, da Tangier. Ayyukan sun bunƙasa yin haƙuri da 'yancin yin tunani da hanyoyin sulhu da ba na rikici ba, da kuma hakkin mata. Shirin ya fahimci cewa idan ana son yaki da sakonnin da ke nuna tsattsauran ra'ayi, to yana da muhimmanci a zabi hanyar da za ta dakile abubuwan da ke kawo tsattsauran ra'ayi.<br>Sauran misalai:<br>• Makarantun Iyaye Mata:Tarbiyantarwa domin Zaman Lafiya (Kungiyar Mata Zalla ta Kasa da Kasa) |
| Karfafa Tattalin Arziki ga Mata da 'Yanmata | Ɗaya daga cikin lamurran da ke kai wa ga tsattsauran ra'ayi shi ne talauci. Wasu hanyoyi da suke masu kai wa ga nasara wajen gina ɗinkakkiyar al'umma a kan yaki da tsattsauran ra'ayi, musamman ga mata, su ne ta hanyar karfafa tattalin arziki. Idan mata na yin magana sosai a cikin al'umma ta hanyar damammaki na tattalin arziki (alal misali, kananan basussuka), za su iya kauce wa ƙungiyoyin da ke neman sauya musu hali a cikin al'ummominsu. | A matakin da aka ɗauka game da hare-haren ta'addanci da aka kai Bangaladash a shekara ta 2005, gwamnati ba sabunta dabarunta na samar da tsaro a kan CT/CVE kaɗai ta yi ba, har da karfafa tattalin arzikin mata. Wannan ya haɗa da ba da ƙaramin bashi ga mata, ƙara zuwa makaranta ga 'yan mata, da kuma masana'antar yin tufafi domin mata. Ta hanyar ilimi da ƙarin damammaki na tattalin arziki, mata da 'yan mata suna da zabi na kauce wa taimaka ma ƙungiyoyin tsattsauran ra'ayi da shigar su.<br>Sauran misalai:<br>• Kungiyar 'Yan uwa Mata Zalla ta Kasa da Kasa (Gudummuwar Mata a Tsaron Kasa da Kasa)<br>• Ku Bari Mu Zamna Lafiya (Paiman Alumni Trust) |

## Karin Bayanai game da Karfafa wa Mata:

- Hanyar Amfani da Jinsi wajen Yaki da Tsattsauran Ra'ayin Rikici:An yi Nasarar Amfani da Darussan da aka koya daga Mata A Gina Zaman Lafiya Da Dakile Rikici a Bangaladash Da Maroko (Brookings)
- Amfani da Jinsi da Yanayin Muhalli wajen Yaki da Tsattsauran Ra'ayin Rikici (CVE):Nazarin Saka Mata da Siffofin Muhalli a Hanyoyin Intanet domin dakile CVE
- Ayyuka Masu Kyau game da Mata da Yaki da  Tsattsauran Ra'ayin Rikici (GCTF)
- MATA DA TSATTSAURAN RA'AYI:KUNGIYAR MATA DA 'YAN MATA TARE DA KUNGIYOYIN JIHADI DA YIN TASIRI GA SHIRI (DFID)
- Mata da Tsattsauran Ra'ayin Rikici a ƙasar Jodan (MATAN MAJALISAR ƊINKIN DUNIYA)
- Fahimtar Rawar da Jinsi ke takawa wajen Dakilewa da Yakar Tsattsauran Ra'ayin Rikici da Ra'ayi Mai Tsauri da ke kai wa ga Ta'addanci (OSCE)
- Bunkasa Rawar da Mata ke takawa wajen Dakilewa da Yaki da Tsattsauran Ra'ayin Rikici (Kungiyar Mata Zalla ta Kasa da Kasa)

## Doka da Bincike

Kari da aiwatar da ayyukan P/CVE fuska da fuska a al'ummomin cikin gida, ƙungiyoyi za su iya samar da bincike a kan P/CVE da jagorancin doka. A ƙasa ga wasu 'yan misalai nan na irin waɗannan ayyuka.

| WURIN AIWATAR DA AIKI | BAYANI | MISALAN FUROJET |
|---|---|---|
| Dubarun P/CVE na Kasa (da matakin jiha/gunduma) | A shekarun baya, ƙasashe da dama sun yi aiki wajen tsara dabarun P/CVE na kasa domin taimaka wa wajen rage tsattsauran ra'ayin rikici. Dubarun sun kebanta ne ga kowace ƙasa, amma da yawansu sun magance matsaloli iri ɗaya da suka ba da gudummuwa wajen taimaka wa ga dakile tsattsauran ra'ayin rikici.  Wasu ƙasashe, kamar Kenya, sun samar da dabarun P/CVE na matakin gunduma domin samar da mai da hankali ga barazanar cikin gida. | Kasashe da dama sun samar da dabarun P/CVE ko kuma sun haɗa da wata dabara a cikin Tsarinsu na Aikin Kasa. Domin samun shiga kowace dubara na waɗannan ƙasashe, duba Rataye na 1 a Jagoran da Ayyuka Masu Kyau na Hedayah: Samar da Dabarun P/CVE na Kasa da Tsare-tsaren Aiki.<br><br>A Kenya, shirin NIWETU an yi shi ne a Dabarun Kasa wajen Yaki da Tsattsauran Ra'ayin Rikici na Kenya sannan yana aiki a matakin gunduma domin haifar da tsare-tsaren aikin P/CVE a gundumomin da ke da haɗari kamar Kwale da Mombasa.<br><br>Babban bayani a kan dabarun P/CVE na ƙasa:<br>• Dabarun CVE na Kasa (Hedayah) |
| Kimanta P/CVE | Kimanta VE wata hanyar bincike ce domin fahimtar lamurran tsattsauran ra'ayin rikici a keɓaɓɓen muhalli. Gudanar da kimantawa ta farko kafin ɗabbaka ayyuka zai iya nuna muhimman sauye-sauyen VE na cikin gida. Saboda haka, za a iya yaɗa wannan bayani zuwa ga tsarawa da ɗabbaka sauran ayyukan P/CVE. | A 2016, Kungiyar Malienne Pour La Survie Au Sahel (AMSS) ta gudanar da nazarin bincike domin gano dalilan da ke kawo tsattsauran ra'ayin rikici (VE) a Mali. Nazarin ya ƙunshi yawon bincike, hira da rukunonin mutane da masu samar da bayanai. An yi nazarin ne a al'ummomi guda biyar– Tombouctou, Goundam, Diré, Niafunké and Rharous –dukkansu suna ƙarƙashin babban yankin Tombouctou. Bbayan binciken da aka yi a kowane wuri, AMSS ta shirya wata tattaunawa da masu ruwa da tsaki na cikin gida domin rarraba sakamako, da tattaunawa a kansa, da kuma tabbatar da shi. Mahalarta sun haɗa da jami'an ƙaramar hukuma, shugabannin CSO, da mambobin al'umma.<br><br>Sauran misalai:<br>• Kaucewar Al'umma daga Bin Tafarkin Tsattsauran Ra'ayin Rikici a Kenya (USIP)<br>• Lamurran da ke Kawo Ra'ayi Mai Tsauri da Tsattsauran Ra'ayin Rikici a Kosovo (ICSVE)<br>• Yaya Jodan take a wajen haɗarin kamuwa da Tsattsauran Ra'ayin Rikici? (IRI) |

## Gyaran Hali da Komawa cikin Al'umma

Gyaran hali da mai da masu tsaurin ra'ayi (R&R) cikin al'umma shi ne abin da kowace gwamnati a duniya ta fi ba wa fifiko. R&R na ɗaɗa zama abu mai fifiko ga al'ummomin cikin gida, wanda ya samu cikas sakamakon dawowar baƙin mayaƙa. A ƙasa ga wasu misalai nan na ayyukan da aka tsara domin gyaran hali da mayar da ɗaiɗaikun mutane a cikin al'umma.

| ENEO LA SHUGHULI | MAELEZO | MIFANO YA MIRADI |
|---|---|---|
| **Ba da shawara, Magance Rauni, da Taimaka wa da bayanan da suka shafi Rauni** | Baƙin mayaƙa da suke dawowa, da ma iyalinsu, za su iya fuskantar rauni na zahiri da/ko rauni na baɗini. A yanayi irin wannan, ba su shawarwari da taimakon ƙwararru a kan rauni zai iya taimaka musu manta abubuwan da suka faru a baya da ba su damar sake komowa cikin al'umma. | Shirin Kumekucha ya ɗabbaƙa Haɗin-guiwar Koren Gida (Green String) a Kenya, shiri ne na gamayyar zamantakewar da al'umma ke jagoranta. Kumekucha wata hanya ce ta aiki tare, wadda ke gabatar da muhimman batutuwa, da suka haɗa da tasirin rauni, hanyoyin rage damuwa, yafiya, warkarwa, sulhuntawa, haƙuri, da mantawa da baya. Kungiyar takan haɗa da labaran al'adu da fasaha daga 'yan Kenya, wanda wannan na samar da yanayi na haƙiƙani wajen fahimar rauni da kuma warkar da shi.<br><br>Sauran bayanai da/ko shiraruwa game da ba da shawara da taimako a kan rauni:<br>• Yadda za a yi Gyaran Halin Masu Tsattsauran Ra'ayin Rikici da Mayar da su a cikin al'umma:Magance Rauni da Rage Abin Kunya (USIP)<br>• Matasa, Rauni da Tsattsauran Ra'ayi (Ci Gaba ba tare da Rikici ba)<br>• Rauni a matsayin abin da ke kai wa ga Tsattsauran Ra'ayin Rikici (START) |

## Damawa da Matasa da Karfafa Musu

Ayyukan P/CVE domin matasa za su iya bambanta, ya danganta da wurin da ake aiwatar da su. Tun da tun asali ƙungiyoyin tsattsauran ra'ayin rikici kokarinsu shi ne ɗaukar matasan da aka tauye wa hakki da saka su aikata rikici, to da yawan shiraruwan P/CVE suna bayyana abubuwan da ke fitar da su daga wannan hali da kuma jin ana damawa da su a cikin al'umma. Shiraruwa da dama da suka yi nasara suna sa ana damawa da matasa kaitsaye a shirin P/CVE. Ta hanyar ƙarfafa wa matasa da mayar da su wakilan kawo sauyi a cikin al'ummominsu, za a iya rage haɗarin shigar su cikin tsattsauran ra'ayin rikici. A ƙasa ga wasu 'yan misalai nan na ayyukan P/CVE da matasa ke jagoranta.

| WURIN AIWATAR DA AIKI | BAYANI | MISALAN FUROJET |
|---|---|---|
| **Karfafa wa Matasa** | Hanya ɗaya ta karfafa wa matasa ita ce ta ba su horo, ilimi da ƙwarewa na su kasance masu kawo sauyi a cikin al'ummominsu. Matasan da ke jin cewa ba su da ƙarfi kuma ba su iya kawo wani sauyi, to za su iya kasancewa an mamaye su sannan an hana su hakkinsu, wannan kuma zai iya kai su ga tsattsauran ra'ayi. Saboda haka, ta hanyar ayyukan da aka yi nufi, matasa za su iya samun ƙwarewa ta jin cewa suna da amfani da tasiri a cikin al'ummominsu. | Daƙile Tsattsauran Ra'ayin Rikici ta hanyar Karfafa wa Matasa a Jodan, Libiya, Maroko da Tunusiya shirin da UNESCO ta dabbaka, wanda ya ƙunshi hanyoyin fannoni da dama. Makasudin shi ne samar da muhallin da za a ƙarfafa wa 'yan mata da matasa, za a saurare su a kuma dama da su a matsayin masu kawo sauyi a cikin al'ummominsu domin daƙile tsattsauran ra'ayin rikici ta: (1) samar wa matasa da kyawawan ɗabi'u, halaye, ilimi da ƙwarewa; (2) bunƙasa sauyi, sadarwa da haɗin kai wanda ya wuce zamantakewa, al'adu, da harsuna; (3) taimakawa wajen damawa da su lamurran mutane; (4) karfafa musu shiga wajen samar da zaman lafiya; da (5) bunƙasa hakkin dan'adam da fahimtar al'adu daban-daban.<br><br>Sauran furojet-furojet game da ƙarfafa wa matasa:<br>• Tabbas Matasa Suna Iyawa (Mercy Corps-Kenya)<br>• Damawa da Matasa wajen Yaki da Tsattsauran Ra'ayi a Nijeriya (IREX) |

| WURIN AIWATAR DA AIKI | BAYANI | MISALAN FUROJET |
|---|---|---|
| Damawa da Matasan da Ba su Aiki ko Wađanda Ba a yi da su | A al'ummomi da dama, matsalar amfani da ƙwarewar da ba ta dace ba tana dađa ƙaruwa a yayin da aka zo maganar rashin aikin yi na matasa. A yanayin irin wannan, ba su da ƙwarewa ta hakika wadda ake nema domin samun aikin da ya dace. Wannan rashin aikin yi zai iya kai wa ga tauyewar rayuwa a cikin al'umma sannan zai iya sa matasa su auka cikin hađarin zama masu tsattsauran ra'ayi. Ta hanyar samar da ƙwarewa ga matasa wadda za ta taimaka musu ga samun aiki, hađarin auka wa zuwa ga tsattsauran ra'ayi zai iya raguwa. | A Philippines, shirin EDC na Ci Gaban Matasan Mindanao (MYDev) yakan yi tayin ƙwarewar da ta shafi rayuwa da horaswa ta samar da aiki ga matasan da ke fuskantar hađarin shiga ƙungiyoyin rikici. Shirin yanuna cewa yana da matuƙar muhimmanci ga matasa saboda yana samar da ƙwarewa mai alfanu. Ta hanyar shirin ne aka gabatar da hađin-guiwar matasa na tsara, masu horaswa, da shugabannin al'umma wađanda ke son kawo sauyi mai kyau. Sun koyi abubuwan da suke sa ran samu daga gwamnati da abubuwan da su ne ya wajaba su yi wa kansu, wanda wannan zai sa su daina jin an ware su da mai da su saniyar ware. Bisa ga rahotannin sojojin cikin gida, ƙungiyoyin tsattsauran ra'ayi sun đakatar da đaukar mutane a wasu birane inda MYDev ke yi ayyuka.<br>Sauran misalai:<br>• Hađakar DRC ga Ayyukan Ci Gaban Matasa (EDC) |
| Jagoranci ko Abu Maikyau | Ushauri au mipango ya kuigwa ni njia bora za kuzuia VE. Kwa kuwaunganisha watu waliojitayarisha kuzuia itikadi kali katika jamii zao, viongozi hawa wanachukuliwa kama watu wenye tabia nzuri ya kuigwa na vijana wanaoweza kushawishika kujiunga na misimamo ya itikadi kali. Watu wenye tabia nzuri za kuigwa wanaweza kuwa washauri wa kitamaduni, lakini wanaweza pia kuwa wanarika na vijana wenzao. Watu wa kuigwa pia wanaweza kuwa waliokuwa wafuasi wa itikadi wanaotaka kuzungumza na wale walio katika hatari ya kujiunga na makundi ya kikatili na kueleza waliopitia. | Karfafar da Kaucewar Al'umma daga Tafarkin Bin Tsattsauran Ra'ayin Rikici a Afurka ta Gabas (STRIVE) na bayar da gudummuwa wajen bunƙasa zaman lafiya, ƙwanciyar hankali da damawa da matasa da shiyoyin da aka mayar saniyar ware a cikin harkokin tattalin arziki na Kenya ta hanyar aiwatar da bincike da ayyuka domin rage tsattsauran ra'ayi da shigar sa. Yi wa matasa jagoranci yana đaya daga cikin manyan ɓangarorin shirin, wanda ke bayar da taimako na kai-da-kai ga matasan da ke cikin hađarin shiga VEOs. Shirin yakan hađa kai da al'ummomin cikin gida a wajen rage tsattsauran ra'ayin rikici ta hanyar ƙara musu ilimi game da dalilai daban-daban da ke sa a fađa cikin rikici ko ƙungiyoyin tsattsauran ra'ayi. Kungiyoyin da shirin ke son kai gare su su ne al'ummomin da ba su da ƙarfi a Kenya wađanda aka dama da su a matsayin jagorori da wađanda aka yi wa jagora, sannan masu ruwa da tsaki suka biyo su.<br>Babban bayani game da Jagorancin Matasa:<br>• Darussan da aka Koya daga Jagorancin Matasa na P/CVE (RUSI) |
| Wasanni da Fasahohi | Damawa da matasa a wasanni da ayyukan fasaha misalai ne na shirin P/CVE. Wasanni, fasahohi da sauran ayyukan al'ada za su iya taimaka wa a tsakanin matasan da ke cikin hađari da tayin tunani na hakika game zamantakewa ko lamurran siyasa ta hanyar shiraruwan da ke da alaƙa. Wađannan ayyuka za su kuma iya taimaka wa wajen samar wa matasa wata manufa mai kyau da hađaka ta ƙwarai da al'ummarsu. | Mnamo Januari 2017, Search for Common Ground ilizindua Mpango wa Kuimarisha Ustahimilivu na Ushirikiano wa Vijana Kupitia Vitabu vya Katuni, mradi wa majaribio wa kujenga ujasiri dhidi ya itikadi kali za kikatili miongoni mwa vijana nchini Tunisia. Mradi huo ulilenga kuwapa vijana ujuzi wa kuunda katuni kama njia mbadala ya kukabiliana na ujumbe unaohimiza vurugu. Mradi huo ulifanya vijana wa Tunisia wawe na sauti. Vijana hao walikuwa na njia chache za kujadili masuala nyeti kama vile itikadi kali. Wengi walipendekeza kubadilisha kitabu cha katuni kuwa msururu wa vipindi, au kufanya maudhui kuwa dijitali na kuwekwa kwa mitandao ya kijamii. Mradi huu ulitoa nakala 4,500 za kitabu cha katuni kinachoitwa Youmiyyat Daly (Siku Katika Maisha ya Daly).<br>Mifano mingine:<br>• Michezo na Usalama (Umoja wa Mataifa) |

| WURIN AIWATAR DA AIKI | BAYANI | MISALAN FUROJET |
|---|---|---|
| Usimulizi wa hadithi | Kuwahusisha vijana kupitia kusimulia hadithi kunaweza kuzibua nafasi nzuri na salama kwa vijana kujieleza, kuimarisha ustadi wa kujieleza, kukuza uhusiano wa kijamii, na huruma - zote ni mbinu muhimu za kuzuia vurugu. Kupitia kwa kusimulia hadithi, vijana wanaweza kueleza mawazo na hisia zao kuhusu mada kama vile vurugu na itikadi kali. | A watan Janairu, 2017, ƙungiyar Search for Common Ground ta ƙaddamar da Karfafar da Kaucewar Matasa daga Tafarkin Bin Tsattsauran Ra'ayi da Damawa da su Ta Hanyar Littattafan Ban Dariya, wani ɗan takaitaccen furojet domin samar da kaucewar matasan Tunisiya daga tafarkin bin tsattsauran ra'ayin rikici. Furojet ɗin ya mayar da hankali ne a kan samar da ƙwarewa ta ƙirƙirar abubuwan ban dariya a matsayin hanyar kauce wa saƙonnin da suke zaburad da rikici. Furojet ɗin ya ɗaga muryoyin matasan Tunisiya waɗanda ke da mafita 'yan kaɗan na tattauna lamurra masu tsantseni irin tsattsauran ra'ayi. Da yawa sun ba da shawarar yin amfani da littafin zanen ban dariya cikin jerin gajerun zane ko mayar da shi na'ura saboda kafafen sa da zumunta. Furojet ɗin ya samar da kwafi 4,500 na littafin zanen ban dariya da aka ba wa suna Youmiyyat Daly (Kwanakin Rayuwar Daly).<br><br>Sauran misalai:<br><br>• Wasanni da Tsaro (Majalisar Ɗinkin Duniya) |
| Bayar da labari | Damawa da matasa ta hanyar bayar da labari zai iya samar da fili mai kyau da aminci wajen bayyana kansu, gina ƙwarewar sadarwa, da samar da alakar zamantakewa da tausayi – dukkan ƙwarewa mai sauki saboda dakile rikici. Ta hanyar bayar da labari, matasa za su iya bayyana tunaninsu da abin da suke ji game da batutuwa kamar rikici da tsattsauran ra'ayi. | A ƙasashe kamar Jodan da Indonisiya, ƙungiyar Search for Common Ground ta ɗabbaka shiraruwa, wanɗanda aka samar wa matasa ƙwarewa ta shirya gajeren fim a kan rayuwarsu, rikicin da suka shiga, da kuma burinsu. Ta hanyar bayar da labaransu da amfani da fina-finansu a bainar jama'a da shiga tattaunawa, matasa za su iya jin ana yi da su kuma suna da ƙarfi a cikin al'ummominsu. Ta hanyar bayar da labari, matasa za su iya ɗinke rarrabuwar da ke akwai, damawa da hukumomin cikin gida da shiga shiraruwan yin sulhu da magance matsala. |